# Ɗan’ Adam

kamar Yadda Allah Ya ke sonsa

Na

**Aminu Isma’il Sagagi**

**Sashe Nazarin Shari’ai**

**Kwalejin Shari’ah Ta malam Aminu kano,**

**Kano**

ABUBWAN DA KE CIKI


**Godiya - - - - ii**

**Shimfiɗa - - - - iii**

**Gabatarwa - - - - 1**

**Su Wance ne mu - - - 4**

**Suffofin da su ka Bambanta**

**Ɗan Adam da Dabba - - - 5**

**Ɗabi' ar Dabba - - - - 6**

**Mutum da son Zuciya - - - 8**

**Mutum a Gidan Gwaji - - - 10**

**Dabarun Yaƙi - - - - 14**

**Harsashin Gina Al'umma (iyaye) - 15**

**Tarbiyyar Addini - - - - - 16ƙ**

**Yanayi Mai Tsafta - - - - 18**

**Nasiha TsakAnin Musulmi - - - 19**

**Dokoki - - - - - - 20**

**Albishirinku Mutane! - - - 24**

## GODIYA

Ina daɗa godiya ga Allah wanda ya ba ni ikon rubuta wannan ɗan ƙaramin littafi, kuma ya ba da ikon sake buga shi karo na biyu.

Ina so na yi amfani da wannan dama na miƙa godiya ta ga Hukumar shari'a ta jihar Kano ƙarƙashin shugabanci sheikh malam Ibrahiam umar kabo, da jagorancin Ustaz Yahaya Tanko, wadda ta ɗauki nauyin sake bugu wannan littafi.

Haka ina godiya ga Shugabana Wali, saboda jagoranci, da tarbiyya da yake yi mana a koda yaushe. Allah Ya saka masa da alheri, amin. Ba zan manta da ɗan'uwa Malam lliyasu Dabo Roni, wanda baya gajiyawa da bugu rubuce- rubucena a kan na'ura mai ƙwaƙkwalwa ba. Allah Ya saka musu da alherinsa, amin.

## SHIMFIƊA

Dukkan godiya ta tabbata ga Allah maɗaukakin Sarki, wanda ya halicci mutum ya sanar da shi yadda zai yi bayani, tsira da aminci su ƙara tabbata ga Mafificin Taliƙai Annabi Muhammadu (Sallallahu Alaihi Wa Sallam). Wanda al'ummarsa ce mafificiya a kan dukkannin al'ummai ba don sun fi kyawun ƙira ba, ba don sun fi tarin dukiya ko ƙarfin mulki ba kuma ba saboda sune shafaffu da mai ba a' a sai domin suna yin umarni da kyakkyawan aiki suna yin hani ga mummuna .

Wannan ɗan littafi "Ɗan Adam kamar yadda Allah Yake Sonsa" na fara buga shi ne tun a shekarar 1997, wato yanzu (2007) shekaru goma ke nan. Kuma a wancen lokaci na fara rubuta shi bayan na gama jami'a da shekara ɗaya, wato akwai ragowar tasirin rayuwar jami'a da ruhinta ke nan.

Saboda a jami'ar "Internation University of Africa" ( I.U.A dake ƙasar Sudan).

Na samu Digiri na farko a Sashin Shari'ar Musulunci, kuma na rubuta binciken neman shaidar digiri a kan yadda za a iya aiwatar da tsarin Shari'ar Masulunci ta hanyar yaɗa kyawawan ɗabi'u (Shari'a and Moral Discipline). Haka kuma a koda yaushe ina da burin na ga al'ummar Musulmi a Nijeriyar suna ɗabbaƙa shari'a a zahiri da baɗinin na rayuwar su gwargwadon iko. Shi ya sa har waƙe da na yi a wancen lokacin naka cewa:

A ƙasar mu yaushe za a ce ba shan giya Dukkan matasa sun la'anci kilaki?

Yaushe Shari' a za ta mamaye ko 'ina A gida da titi har da tsarin mulki.

Irin wannan kishi da karsashi na matashi sabon fitowa daga jami'a ya sa daga dawowata gida Nijeriya, sai na dinga ji a raina kamar in an ƙyale ni zan iya kawo gyara a ƙasar baki ɗaya cikin ƙaramin lokaci. Haka

ne ya sa a wancan lokaci na je na shirya wani jadawali na ayyukan wa'azi wanda na tsarashi a kan yadda a cikin shekara biyu (1997 – 1999) za a iya ɗabbaƙa shari'a jihar kano.

________________

Duban Littafi Ajiyar zuciya. Na Aminu isma'il Sagagi, waƙa mai taken: Dogon buri.

A wancan lokaci na gabatar da wannan Manhaja ( ko jadawali) ga shugabannina a ƙungiyar Mu'assasah (Islamici foundation of Nigeria ), ina iya tunawa da yadda Marigayi Malam Ibrahim Bello Ringim (Allah ya jiƙansa) ya yi ta dariya, ganin cewa na zo da irin abin mu na ƙuruciya. A cikin ƙoƙarin cimma wannan buri ne na shiga rubuta wasu 'yan takardu ( hand bills), waɗanda ƙungiyar ta Mu'assasah ta ɗauki nauyin bugawa, kamar: Tsarkin Harshe, da kuma kyawawan Ɗabi'u a Musulunci (ita kuma wata makaranta ce a kaduna ta ɗauki nauyin buga ta). Sannan na nemi haɗin kan Shugabana Sheikh Na'ibi Sulaiman Wali a kan gudanar da wasu shirye – shirye guda biyu; na farko da sunan Mu'assasah muka tuntuɓi Shugaban ƙungiyar Direbobin Haya, domin su hana direbobin Bus da 'yan Taksi liƙa hotunan mata tsirara a motocin nasu.

Shiri na biyu kuma, shi ne na haɗa kai da gidan Rediyon kano ta hanyar Malam Abubakar Darma, inda na dinga rubuta wasu maganganu na faɗakarwa, shi kuma ya sa ake dinga karantawa a matsayin talla, (wanda ake dinga sanya wa akai – akai) kaɗan daga abubuwan da faɗakarwar ta ƙunsa sun haɗa da: kira a kan neman ilimi da Nasiha a kan maƙotaka, da sauransu.

Bayan wannan sai na rubuta wannan littafin mai suna "Ɗan Adam kamar Yadda Allah Yake sonsa" wanda a ciki a ka yi ƙoƙarin nuna matakai da hanyoyi waɗanda tabbas in aka gwada su, to cikin sauƙi za a iya aiwatar da Shari'a matakin abin da ɗaiɗaiku su ka sa kansa. Matakan sun haɗa da, samar da ma'aurata masu bin Allah, da kuma tarbiyyar yara irin ta Musulunci, da ƙoƙarin tsaftace gari daga ayyukan assha da na masha'a,

yadda matasa ba za su dinga ganin abin da zai kwaɗaitar da aikata mummunar ɓarna ba.

Da kuma samar da 'yan sandan Ɗa'a[2] waɗanda za su bazama cikin gari domin yin gargaɗida nasiha ga mutane cikin girmamawa da tausa sawa, ga wanda ya cancanci haka.

Ko da yake ban iya tanadar isassun kuɗin da za a bugu littafin ba, sai na nemi wani matashi a Unguwar ƙwalwa, shi kuma sana'ar sa ke nan, sai na ba shi haƙƙin mallakar littafin.

______________

[2] 'Yan Hisba ke nan, amma na kira su da sunan 'Yan sandan Ɗa'a saboda a wancan lokaci (1997) ba a fara aiwatar da Shari'a ba, wanda Gwamnatin jihar Zamfara ta fara a (2000). Mafi yawan mutanen gari ba su saba da kalmar Hisba ba.

Domin dai a samu a buga shi. Kuma haka ɗin aka yi, amma sai dai bugun bai yi kyau ba, kuma kwafi dubu ɗaya kawai aka buga.

Kasancewar duk da haka littafin ya ƙare, shi ne na sake ƙoƙarin buga shi, kuma ko da yake ban yi wasu sauye – sauye mai yawa a cikinsa ba, amma ina kyautata zato in Allah Ya yarda zai bayar da amfani. Ina roƙon Allah ya ba mu ladan duka irin waɗannan ayyuka, kuma ya yi mana afuwa da gafara gare mu da iyayenmu, amin.

**Aminu Isma'il Sagagi,**

**Sashen Nazarin Shari' ar Musulunci,**

**Kwalejin Shari'a Ta Malam Aminu Kano,Kano.**

**(09/03/07)**

## GABATARWA

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai jinƙai.Dukkan yabo da godiya ya tabbata ga Allah wanda ya halicci ɗan' adam "mutum", kuma ya fifita shi a kan mafi yawan halittun sa fifitawa.

Tsira da amincin Allah su tabbata ga Shugaban halitta Annabi Muhammad (Sallallahu Alaihi Wasallam ), wanda Allah ya aiko shi domin tsamar da mutane daga halaka, da bambanta rayuwarsu daga ta dabba, duk da Alayensa da Sahabbansa baki ɗaya. Bayan haka, yayin da na duba littafin "**Ɗan Adam Kamar Yadda Allah Ya ke Son sa**" wanda ɗan'uwa Malam Aminu Isma'il Sagagi ya wallafa shi, sai na ga yanda muhimmanci da ƙima, musamman ma ga matasan Musulmi, mazansu da matansu.

Saboda rayuwar ɗan' Adam ingantuwarta da lalacewarta gaba ɗaya, tana dangantuwa ne ga ingantuwa da lalacewar samartakarsu. Don haka yara matasa masu sha'awar rayuwa, waɗanda ba sa iya banbance rayuwar ɗan 'Adam da ta dabba idan suka karanta littafin nan kuma suka fahimce shi yadda ya kamata suka yi amfani da abin da ke ciki na tabbata za su rubauta, kuma da iyaye sun ji daɗin, al'umma sun huta. Da irin waɗannan littattafi za su yawaita za mu nisanci riyuwar Turai marar amfani, wadda ba ta da bambanci da rayuwar dabba.

Ina kira ga Malamai da 'yan'uwa almajirai su yi koyi da wannan bawan Allah, ɗan'uwa Malam Aminu domin irin waɗannan littattafi su yawaita, musamman ya kasance ya dace da matakan da Malamin ya bi wajen futo da mutum, yanayin rayuwarsa, dabba yanayin rayuwarta wajen nuna bambancin tsakaninsu, fifikon da mutum ke da shi a kan dabba da abubuwa kamar haka:

- Tsarin rayuwar ɗan'Adam.
- Abincin ɗan'Adam.
- Auratayyar ɗan'Adam.

- Dangantaka tsakanin ‘yan’ Adam.
- Hankalin dan’Adam.
- Ilimin dan’Adam.
- Arziƙin dan’Adam.
- Matsugunin dan’Adam.

Duk da wannan fifiko da ɗan’Adam ke da shi, idan bai rayu yadda Allah ke buƙatarsa ba, sai a fifita dabba a kansa. Allah Ya kiyaye, ameen. Allah Ya sakawa Malam Aminu Sagagi da alkhariinSa, ya nauyaya mar.

Allah Ya yi daɗin tsarin da amincinsa ga Annabi Muhammadu (Sallallahu Alaihi Wasallam) da Alayensa da Sahababbansa, ameen.

**(Muhammad Yusuf)**

**(1997)**

## SU WANE NE MU?

Mu halitta ce ta jinsin mutane, kuma muna daga cikin waɗanda Allah bai halicce su domin komai ba, sai domin su bauta masa kawai, saboda haka Ya ba mu hankali don mu yi ilimi, da shi ne za mu san dai - dai kuma mu san abin da ba dai - dai ba, mu san gaskiya daga ƙarya, mu gane bambancin shiriya da ɓata. Da haka za mu iya yin aiki na gari mu kuma nesanci miyagun ayyuka.

Mutum cikakke shi ne wanda ya yi imani da Allah da Manzo Sa, kuma ba ya rabuwa da yin managarcin aiki, idan a ka samu saɓani, ya yi tuntuɓe, ya aikata kuskure, sai ya yi sauri ya tuba ya koma ga Allah , saboba shi mai imani ne da Allah, kuma mai yin koyi da Manzon Allah (Sallallahu Alaihi Wasallam).

Wannan ita ce siffa ta cikakken mutum, a mahangar Musulunci. Ba kawai kasan cewarsa mai ɗauke da kai da ƙafa da iya magana, da dariya ba ya zama dole sai ya haɗa waɗannan siffofi sannan zai amsa sunansa **Ɗan'Adam.** Daga nan ne idan an yi tambaya: "Su waye mu" Za mu cancanci bayar da amsar: "Mu mutane ne".

## SIFFOFIN DA SUKA BAMBANTA MUTUM DA DABBA

Abubuwan da ke sawa mutum ya sami tsira (a dunƙule) guda huɗu ne, kamar haka:

- *Imani:*
- *Aiki na gari;*
- *Umarni da kyakkyawan aiki da hana mummunan aiki;*
- *Koyawa juna haƙuri da juriya.*

Wato ya kamata ya zama mai kintsa kai da shiryar da shi, tare da shiriyar da sauran mutane da nuna musu duk abin da zai amfana musu duniya da lahirarsu.

## DABI’AR DABBA.

Dabba, kalma ce ta Larabci, ta na nufin halittar da ke taka ƙasa, wato halittu masu rai ke nan. Amma galibi idan a ka ce (dabba) to, ana nufin sauran halittu marasa hankali, kamar jaki da kare do doki da dai sauransu.

Babban abin da aka san dabbobi da shi; shi ne rashin hankali irin na mutane, kuma da rashin iya sarrafa al’amura bisa cikakken zaɓi na turanci da ilimi, duk da yake ana samu wasu dabbobi masu baiwa ta hazaƙa a wasu fannonin rayuwa iri- iri, amma duk da haka matsayinsu ƙasa ya ke da na mutane saboda cikakken hankali da Allah Ya ba su tare da Wahayi ta hanyar Manzanni, abin da ka iya jagorantarsu su bi tafarkin shiriya tsantsa.

Dabbobi ba su da wata manufa ta musamman da suke iya zaɓawa kansu a rayuwa, mafi muhimmancin abin da ke gabansu shi ne ci da sha da Barbara.

Lallai ne mutum ya ɗinga faɗaka daga al’amuransa na yau da gobe, domin ya tabbata yana tafiyar da su akan tafarkin Imani da kuma aiki da hankali, domin idan ya sake ya zama shima ba shi da manufa sai dai ci da sha da sauransu. To sai ya fi dabbobi lalacewa. Allah Ya kiyaye mu, ameen.

## MUTUM DA SON ZUCIYA.

Zuciya ita ce matattarar buri da kwaɗayi da sha’awa gurin mutum, kuma ita babu ruwanta da ba dai-dai ba, abin da duk ya ƙayatar da ita za ta so shi, ko ya dace ko bai dace ba, kamar kare ta ke, abin da duk da ya so ya bi zai bi shi a guje don ya kama, ko ya yi gyara ko ya yi ɓarna, wata ran ya ciji ɓarawo, wata rana kuma ya ciji baƙon masu gida. Amma domin a amfana da gyaransa kuma a tsira daga ɓarnarsa shine uban gidansa yake tsawatar masa in ya ga zai ciji wanda bai kamata ba, ko ya saka masa

sasari da sarƙa, don ya hana shi ɓarna, to haka zuciya ita ma sai da tsawatarwa.

Saboda haka, hankali shi ne linzamin zuciya, shine mai yi mata dabaibayi domin kada ta shige gona-da iri. Shi kuma Imani shine alƙiblar hankali. Imani shine ya san lokacin da ya dace a saki ragamar zuciya, da kuma lokacin da ya dace a saka mata waigi.

Ashe, da za a ƙyale zuciya da abin da take so babu tsawatarwa, kuma babu kyakkyawan tunani, to da zuciya ta yi katoɓara marar misali, kuma ka baiwa mutum (marar lafiya) ruwan sikari da ruwan magani mai ɗaci, zuciyarsa sai ta fi son ruwan sukari, amma kyakkyawan tunani shine zai nuna masa cewa magani duk da ɗacin da yake da shi shine mafi amfani ba ruwan sikari ba komai zaƙinsa.

**MUTUM A GIDAN GWAJI (DUNIYA).**

Allah Maigirma da Ɗaukaka ya bayyana cewa: *"Shi ne wanda ya halicci mutuwa da rayuwa domin ya gwada ku. Wane ne mafi kyawun aiki a cikin ku"* (Suratul Mulk: 2). Kuma manzon Allah (Sallallahu Alaihi Wasallam) ya siffanta Aljanna da haja. (Kayan sayarwa) mai tsada, ba a samunta a ɓagas sai an yi aiki mai kyau, aiki na gari, sannan za a iya mallakarta.

Don haka ne Allah Ya sauko da mutum a gidan duniya, sai Ya jarraba shi da shaiɗan wanda kullum aikinsa shine;ya ɓatar da mutum, ya afka shi cikin saɓo. Wato ya sa shi ya faɗi a jarrabawa!

Bugu da ƙari, shi shaiɗan yana da mataimaka masu taya shi aikin ɓatar da mutum, waɗannan mataimaka suna da yawa, amma mafi hatsari a cikinsu suna:Son zuciya da ruɗin duniya. Saboda haka, idan mutum yana son ya ci jarrabawar Allah ba shi da hanyar da ta wuce saɓawa waɗancan magauta guda uku.

- Shaiɗan;
- Son zuciya;
- Ruɗin zuciya

- **Saɓawa Shaiɗan:** Ka da mutum ya manta da ƙiyayyar da shaiɗan ya ke yi masa, don haka ya kamata ya dauwama akan neman tsari da shi, sannan ya riƙe koyarwar Musulunci sosai.
- **Saɓawa Son Zuciya:** Ta hanyar bin ƙa'ida, da riƙe gaskiya da tsarin amana, ko da ransa ba ya so.
- **Saɓawa Ruɗin Duniya:** Ta hanyar neman halal, da haƙuri da abin da ya samu ta hanyarsa, ka da ya yi garajen tara kayan more rayuwa ta hanyar sata da zamba

Domin haka mutum a gidan duniya kamar a filin kokawa ya ke,

abokan karawarsa su ne shaiɗan da son zuciya da ruɗin duniya, wanda ya yi jarumta ya nana su da ƙasa, to shi ne zai ci kambu kuma shi ne wanda zai zama jarumi, gwarzon maza (ko kuma jarumai mata!)

Domin haka ne Allah Ya aiko da Manzanni suka bayyana dokoki, suka ajiye ƙa'idoji, suka tsara hanyoyi, suka shata iyakoki. Mutumin da ya tsaya idan aka tsayar da shi, ya kuma nufi inda a ka umarce shi shine wanda ya kayar da waɗancan abokan kokawa tasa, kuma shi ne ya ci jarrabawa, don haka sakamakonsa shi ne samun dacewa da yardar Allah. (Allah Ya sa mu dace) Ameen.

Idan mutum ya yi tunani, zai gane cewa, yin haƙuri a cikin bin Allah, da kuma yin dauriya wajen saɓawa son zuciya ba a cikin shari'ar addini kawai yake ba, a'a har ma cikin shari'ar rayuwa. Akwai abubuwa da baya so, amma haka yake haƙura ya tafi yadda aka tafi da shi a cikinsu. Ba a komai ne zai gudanar da rayuwarsa yadda ya ke so ba, kamar tsufa da rashin lafiya da mutuwa waɗanda ba shi da tasiri a kansu. To, haka ma a cikin bin shari'ar addini, sai ya haƙura ya bi doka ko ta yi masa daɗi ko ba ta yi masa ba, kamar yadda ya saba yi, a shari'ar rayuwa. Abu dai mafi muhimmanci wanda yin tunani a kansa zai taimaka mana wajen ƙara yin haƙuri cikin bin Allah shi ne, duk abin da shari'a ta umarce shi da shi, to wannan abin amfani ne da alheri gare shi, a duniya da lahira, kuma duk abin da shari'a ta haramta masa, to sharri ne a gare shi da masifa da ƙangi da shiga halin ƙaƙa-naka-yi. Allah Ya kiyashe mu, ameen.

Duba ka gani; Allah Ya wajabta yin Imani da shi (Allah Shi kaɗai, wanda ba shi da abokin tarayya, mai iko ne bisa komai. wanda ya halacci dukkan halitta).kuma ya haramta imani da yin bauta ga wani wanda ba Shi ba, ko Mutum ko Aljan ko Mala'ika ko tauraro ko Rana ko Wata ko Dutse ko itace, da sauransu. Wanda ya ke dukkansu samar da su Allah Ya yi gajiyayyu ne mubuƙata ne ba su da ikon yin wani abu sai da izinin Allah.Ka ga a nan wanda ya yi aiki da umarnin Allah shi ne zai amfana, saboda zai samu nutsuwa a rayuwarsa. Wanda ya saɓa masa kuma shi ne zai cutu domin zai rayu cikin ruɗani, da damuwa.

Haka kuma, Allah Ya halatta madara da zuma, amma ya haramta giya, kuma ya halatta ciniki da saye da sayarwa na ƙa'ida,amma ya haramta cin kuɗin-ruwa da caca da cin-hanci da sata. Haka kuma Allah ya halattawa mutum ya yi aure daga mace ɗaya zuwa huɗu, amma Ya haramta zina. Allah Ya halatta zaman lafiya,, zumunci, da mutunci, da alheri, da ƙaunar juna, amma Ya haramta gaba, da ƙullata, da kinibibi, da munafunci, da ƙeta, da dai kowane mugun hali. Dukkan abin da Allah Ya halatta mana alheri ne garemu, kuma dukkan abin da ya haramta mana sharrine. Allah Ya sa mu gane, ameen.

**DABARUN YAKI.**

Mutum yana daga cikin ƙananan halittun Allah, kuma raunana, marasa buwayayyen ƙarfi,hatta a mahallinsa mutum ɗan-tsurut ya ke in an kwatanta shi da sauran halittu maƙwabtansa, kamar duwatsu da bishiyoyi da raƙuma da jakuna da shanu da sauran manyan dabboni, amma duk da haka sai Allah Ya ba shi hankali da dabara, kuma da su ne yake cin galaba a kan manyan halittu waɗanda suka fi ƙarfinsa. Yana yin haka ne ta hanyar haɗin kai (taron dangi ) da samar da kayan aiki (makamai da aloli) tare da bin matakai na sauƙaƙe wahalhalu. Wato mutum baya fitowa shi kaɗai da fararen tafukan hannunsa ya tunkari giwa ko dutse, in ya yi haka, sai a gama da shi! Kamar haka idan mutum ya tsaya shi kaɗai ba tare da waɗansu makarari ba, ya fuskanci son zuciya da shaiɗan da ruɗin duniya, to lallai zai sha mamaki, domin kuwa ba zai kai labari ba. Lallai sai ya yi shiri kuma ya tanadi dabarun yaƙi. Babu shakka bin waɗannan dabaru yana taimakawa ƙwarai, idan a ka gamu da muwafaƙa daga Allah. Dabarun sune kamar haka:

- Harsashin gina al'umma (iyaye).
- Tarbiyyar addini.
- Yanayi mai tsafta.
- Nasiha tsakanin Musulmi.

- Dokoki.

- **Harsashin Gina Al'umma (Iyaye):**

  Samuwar mutum daga iyaye masu addini shi ne babban harsashin da za a gina kyawawan halaye da ayyuka na gari a kai. Kasancewar mutum ya riga ya gado wannan ɗabi'a ta addini daga mahaifa, hakan zai sanya shi bin dokokin addini ba tare da jin takura mai tsanani ba. Saboda haka mutumin da ya siffantu da halin addini zai yi wa maƙiyansa waɗan da aka faɗa a baya wuyar ɓatarwa. Kuma saboda haka ne addinin Musulunci ya zaɓawa mutum mace ma'abociyar addini wadda aka tabbatar da cewa ta fi mace mai dukiya ko mai kyau ko 'yar dangi, matuƙar ba su da addini. Kuma saboda haka Manzon Allah (Sallallahu Alaihi Wasallam ) ya umarci waliyyan (ma'aura) mata da cewa; da zarar wanda kuka yarda da addininsa (ya zo muku ) to ku aura masa. Babu shakka yin auratayya tsakanin mace da miji ita ce hanya mafi sauƙi wajen samar da mutum mai biyayya ga Allah ba tare da gumin goshi ba.

- **Tarbiyyar Addini.**

Duk da muhimmanci samun mutum daga iyaye masu addini, wannan ba zai wadatar ga barin yi masa tarbiyya irin ta addini ba. Ita tarbiyya gini ce akan harsashin da iyaye su ka kafa, ta zamowar su masu addini. Ko da yake tarbiyya (idan a ka dace) za ta iya gyara mutumin da bai gaji halin addini daga iyayensa ba, amma mafi yawan lokaci, tarbiyya ga wanda ya gaji halin addini ta fi sauƙi da tasiri. Saboda haka wajibi ne ga mai shirin yin aure mace ko namiji ya fi bayar da muhimmanci ga siffar addini a wurin wanda zai aura fiye da kowace irin siffa daban. Sai dai ida halin addini ya haɗu da sauran halaye, ko siffofi, kamar kyawun halitta da dukiya ko dangi da sauransu, to haka ya fi kyau, idan kuma aka sami dukkan siffofi sun haɗu, sai dai babu addini shi kaɗai to abu ya ɓaci, lallai ne a nemi mai addini.

Sannan kuma ita kanta tarbiyyar addini ba za ta yiwu cikin sauƙi

ba, sai idan mahaifa masu addini ne, domin sune masu tarbiyya na farko,yana da kyau musan cewa ita tarbiyyar addini ana fara yiwa yaro ita tun kafin a haife shi ta hanyar aiwatar da ladubban da addini ya tanadarwa miji da mata, waɗanda idan suka bi su, babu shakka albarkar yin haka za ta shafi ɗan da za su haifa. Haka kuma ba za ta samu ba daga mahaifa bin tsarin rayuwar Yahudu da Nasara, waɗanda ba ruwansu da addini.Misalin, Manzo Allah (Sallallahu Alaihi Wasallam)yace: "*idan mutum zai kusanci iyalinsa ya yi addu'a ya roƙi Allah Ya kiyaye su (Shi da matar) daga shaiɗan, kuma ya nesantar da shaiɗan daga abin da za su Haifa".*Manzo Allah (Sallallahu Alaihi Wasallam ) yace : idan aka samu yin hakan kafin kusanta, Allah zai kare shi daga shaiɗan.

Lallai babu shakka irin wannan ɗa an fara yi masa tarbiyya ta addini tun kafin a sami cikinsa.

Haka idan a na maganar tarbiyyar addini, lallai ne a tsaya akan batun karatu, domin shi ne tushen tarbiyya, don haka kowacce irin makarantar da yaro zai shiga ya kamata a tabbata makaranta ce wandda ta ƙunshi koyar da karatu tare da koyar da tarbiyyar addinin Musulunci, kamar yadda Allah Ya saukar kuma Manzo Sa (Sallallahu Alaihi Wassallam ) ya isar. Haka kuma abokin karatun yaro ko abokin hirarsa, shirye-shiryen talabijin da na rediyo da rikoda da inji mai ƙwaƙwalwa ( *computer)* duka lallai ne ya yi masa jagora don ya yi amfani da abin da zai haɓaka tarbiyyarsa ba wanda zai rusa ta ba. Idan aka yiwa mutum haka babu shakka an taimake shi, domin zai iya cin jarrabawarsa cikin sauƙi. Kuma zai gagari abokan gabarsa (shaiɗan da ruɗin duniya da son zuciya).

- **Yanayi Mai Tsafta.**

Daga cikin abin da ke sauƙaƙawa mutum aikata kyawawan aiki shine yanayin gari mai tsafta, wato ya kasance duk abin da mutum ya dosa a gari ba zai ga abin da zai kwaɗaita masa saɓon Allah ba. Babu tsiraici barkatai, babu ƙaɗe-kaɗe da waƙe-waƙen batsa da fajirai, babu liƙe-liƙen assha, babu shirye-shiryen lalata da fitsara a rediyo

da talabijin da jaridu da kasa-kasai. Irin wannan yanayi wajibi ne Shugabannin Musulunci su samar da shi ko ta halin ƙaƙa, domin talakawansu(Musulmai) su sami yanayi mai kyau wanda za su bi Allah a cikinsa ba tare da tashin hankali ba.

- **Nasiha Tsakanin Musulmi.**

Yin nasiha ga Musulmi a junansu wani babban tsaro ne ga imanin Musulmi, ɓarna ba ta yaɗuwa a inda nasiha take aiki, saboda a na murƙushe ta ne tun tana garwashi kafin ta gagara ta zama gobarar daji.

Duk inda mutum ya ga ɗan'uwansa yana aikata, ko furta wani abu marar kyau, wanda ya saɓawa umarnin Allah (Subahanahu Wata'ala) ƙarara, to lallai ne wannan mutum ya yi nasiha ga wannan ɗan'uwa nasa ta hanya mai kyau, har sai ya tsamo shi daga halaka. Haka idan ya ga ɗan'uwansa ya taƙaita ga barin aikata wani aiki ko wani hali na kirki, to aikinsa ya yi masa nasiha har sai ya dawo da shi, don ya aikata abin da Allah yake so, kuma mutum zai iya yiwa sauran al'umma nasiha ta hanyar yi musu adalci tare da kyautata aikinsa, ko sana'arsa don amfanin jama'a ba tare da cutar da su ba.

Sannan kuma ya kamata a gane cewa ita nasiha, idan aka yi ta tsakani da Allah, to ba sai lallai wani muhimmin mutum kawai zai yi ta ga sauran jam'a ba, a'a tsakanin Uba da ɗa da wa da ƙani, da mata da miji da shugaba da talaka da ubangida da yaron gida, kowa yana iya yiwa kowa nasiha cikin ladabi da girmamawa, da neman yardar Allah. Da haka ne mutane za su taimaki kansu-da kansu, su taya juna biyayya ga Allah.

- Dokoki.

Daga cikin abin da ke taimakawa mutum a kan biyayya ga Allah, da

kuma saɓawa son zuciya, har da kafa dokoki waɗanda za su toshe ƙofar saɓon Allah da kafa waɗanda za su ɓullo da hanyoyin bin Allah a rahusa (cikin sauƙi).

Wannan aiki ne na shugabanni tare da sauran jama'ar gari baki ɗaya, wato lallai ne shugabannin su kafa doka, kuma su tsare ta, duk dokar da za su kafa su tabbata wadda ta dace da umarnin Allah ce, kuma duk dokar da ta saɓa umarnin Allah lallai ne su kawar da ita kowa nene ya zo da ita, domin idan Allah Ya ba da umarni, wani mutum ya soke umarnin Allah, su ka bi na wannan mutum, to babu shakka sun fifita shi a kan Allah, kuma duk ranar da Allah Ya kama su, shi ba zai iya ƙwatarsu ba Allah Ya gafarta mana., ameen.

Kuma aikin mutanen gari ne da su nemi shugabannin su, a kan su aiwatar musu da dokokin Allah (Subahanahu Wata'ala) kuma su kawar da duk wata doka da ta saɓawa umarnin Allah, sannan su taya shugabannin nasu a kan haka ta kowace hanya shari'antacciya.

Daga cikin dokokin da ya kamata a kafa su ne: Haramtawa Musulmi shan giya, sayar da ita da ɗaukan dakon ta, da bayar da hayar gidan ta, ko tallanta da haramta karuwanci da duk abin da zai taimaka a yi shi, kamar bayyana tsiraici da cuɗanyar maza da mata a wuraren taro da makarantu, da abubuwan hawa, da kaɗaitar namiji da mace marar dalili da tsananta harkar aure da sauransu.

A taƙaice a tanadi dokokin da za su hana dukkan miyagun ayyuka, irin su cin riba da caca da sauransu.

Sannan su yi umarni da dukkan kyawawann ayyuka, kamar ba da zakka da ayyukan ibada baki ɗaya.

Na san wannan aiki ne ja-ja-jir, amma meye aikin mutum a duniya idan ba jan aiki ba? Don haka lallai ne mu zage dantse mu tunkari kowane aiki mai kyau mu kuma tuna da cewa Allah zai taimake mu a kan kowane aikin alheri. Allah Ya sa mu dace ameen.

Don a samu sauƙin aiwatar da waɗannan dokokin. Sai an tanadi 'yan

sandan ɗa'a, waɗanda za a basu cikakken horo na yadda za su yi horo da kyakkyawan aiki da hani ga mummunnan aiki, waɗanda za su bazama cikin gari a ko ina, idan sun ga ana saɓawa dokar Allah sai su kare ta ta hanyar ilimantarwa, ko tsawatarwa ko kamawa tare da gurfanarwa a gaban shari'a.

Abu na gaba mafi mahimmanci, kuma wanda zai sauƙaƙe aiwatar da dokokin Allah shi ne tanadar manhajar ilimi ingantanciya wandda za ta fitar da muminin bawa, salihi, managarci , mai tsoron Allah, sai a tanadi wannan manhaja don aiwatar da ita a dukkan makarantu na boko da na allo, da na islamiyya.

Tsarin ilimantarwa da tarbiyyantarwa ba zai tsaya kan yara ko ɗalibai kawai ba, a'a har da dukkan jama'ar gari , kowanne a tanadi hanyar da za ta dace da matsayin hankalikansa da kuma iliminsa don ɗora mutane akan ayyukan imani da tsarkake zuciya, da neman ilimi don samun yardar Allah.

Sai da haka ne, sannan doka za ta yi tasiri, amma don an kafa doka kawai, kuma, an yi shelarta, wannan ba zai yi tasiri ba a al'ummar da ta daɗe tana cin karenta babu babbaka karƙashin tsarin da yake ta halatta shan giya da zina da caca da kowace irin kaba'ira.

Daga nan idan muka yi nazari mutum wanda aka Haifa daga iyaye masu addini, sannan ya sami tarbiyya mai kyau ta addini,ku ma ya rayu tsakanin mutane masu yiwa juna nasiha, kuma a cikin al'umma wadda take da dokoki masu tsare martabar addini, babu shakka za mu ga an sami mutum na gari wanda ya yi sa'ar samu kansa cikin mutane waɗanda za su taimake shi, su taya shi yin aikin da Allah Ya halicce shi dominsa, ba mutanen da za su yi ko'oho da shi, ko kuma waɗanda za su taya shaiɗan aikin ɓatar da shi da ƙarfi da yaji ba.

**ALBISHIRINKU MUTANE!**

Allah ya yiwa mutane albishir da cewa; idan suka yi mani da Shi suka ji tsoronsa, to zai buɗe musu arziƙi da albarkatu sama da ƙasa, wannan tun daga duniya ke nan. A lahira kuma za su gamu da Rahamar Allah, kuma zai sanya su cikin Aljanna mai Ni'ima.

Don haka, mutane su farka daga barci su tashi tsaye wajen gudanar da rayuwarsu kamar yadda Allah Ya umarce su, su manta da ruɗin shaiɗan da ruɗin duniya waɗanda suke hana biyayya ga Allah, suke angizasu ya zuwa saɓon Allah ta hanyar bin soye-soyen zukatansu

Allah Ya gafarta mana, kuma Ya ba mu muwafaƙa, ameen.

Aminu Isma'il Sagagi (1997)

Zubairu Bello mosque.

Opposite Zoo Road,

Kano.